(١)

## MATSAYIN GIRMAMAWA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Lallai kai ɗin nan mai riƙo ne da kyawawan sifofi da kyawawan ayyuka da Allah ya halicce ka a kai)** [al- Ƙalam: 4]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai riƙo da kyawawan ɗabi’u masu daraja da girma, muhimmin ginshiƙi ne cikin ginshiƙan gina ƙasashe da cigaba, ba zai taɓa yiwuwa a gina cigaba mai ɗorewa, ta kuma tabbata, ta kuma tsera wa sa’o’i ba, ba tare da an gina su akan kyawawan ɗabi’u, da nagartattun tadodi ba, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ya ku al'umman Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa alihí wa sallam), ku ne mafifitan al'ummomi da Allah Maɗaukakin Sarki ya halitta domin amfanar mutane, matuƙar dai kun kasance kuna yin umurni da aikata alhairi da ɗa'a, kuna kuma hana aikata saɓo, kuna kuma yin ingantaccen imani da Allah, imani na gaskiya)** [Ali Imran: 110].

Tabbas duk wani haɗin kai, da ƙara samun ƙarfi da za a samu tsakanin al’umma, suna zuwa ne ta hanyar mutunta kyawawan ɗabi’u, da aiwatar da su a aikace, alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa:

"Al'ummomi ba wasu abubuwa ba ne da suka wuce tari kyawawan ɗabi'u, da zaran an rasa kyawawan ɗabi'u, to su ma an rasa su kenan".

Babu shakka ɗabi'ar girmamawa tana cikin waɗannan muhimman kyawawan ɗabi'u na mutuntaka masu daraja, wadda addinin Musulunci ya y i kira zuwa gare su, ɗabi'a ce da kowane mutum yake fata ya zama yana da dangantaka da ita, a kuma riƙa sifanta shi da ita a koda yaushe, lallai addininmu mai daraja ya yi kira da a sifantu da wannan ɗabi'a ta dukan fuskokinta, kaman irinsu: girmama kai, ta yanda mutum zai kiyaye mutuncinsa, ya katange kansa daga aikata duk wani abu da zai kai shi zuwa ga zargi, gami da aibatawa, dole ne ya nesanci wuraren da suke da shubuha, ko yiwuwar a tuhume shi da wani abu mara kyau, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya ji tsoro auka wa shubuhohi, to babu shakka ya tseratar da addininsa da mutuncinsa..)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Sam bai kamata mumini ya ƙasƙantar da kansa ba)**, Alƙali al- Jarjaniy yana cewa:

"Har yanzu fa ina nan ina killace mutunci na a gefe ɗaya daga barin duk wani abu da yake kawo ƙasƙanci, na zaɓi in ribaci kiyayewa.. Sukan ce mini: za a iya samun ruwa a nan, ni kuma na ce masu: ni ma na gani, amma dai 'yantacciyar zuciya ta ta zaɓi ta jure wa ƙishirwa.. ba kowace walƙiya ce idan ta wulƙa take iya jan hankali na ba, ba kuma kowane wanda yake rayuwa a bayan ƙasa ne na yarda ya zama mai taimako na ba".

Wani mawaƙi yana cewa:

"Zan iya cin ƙurar ƙasa akan a gan ni ina tozartar da kai na wajen roƙon wasu".

Antar al- Absiy yana cewa:

"Na kan ga ganima a gaba na, ta yanda idan na so zan kwashe ta, amma kunya, da mutunci na sai su hana ni".

Haka ma: Girmama wanda muke da saɓani da shi a wurin addini, da ƙabila, ko al'adu, ta hanyar mutunta haƙƙoƙinsa na rayuwa, da na ma'ana, lallai wani na yana da haƙƙin girmama jikinsa, da dukiyarsa, da duk abubuwan da ya mallaka a kai na, dole ne in mutunta 'yancinsa, da karamarsa, da aƙidarsa, shi addinin Musulunci addini ne da yake girmama ɗan Adam, ya kuma mutunta shi, yana kuma kira da a mutunta shi, a kuma karrama shi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai tabbas mun karrama ɗan Adam..)** [al- Isra'i: 70], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Shi al'amarin addini babu tilastawa a cikinsa)** [al- Baƙra: 256], Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Allah ba ya hana ku girmama da sada zumuntanku da kãfiran da ba su yaƙe ku ba, ba kuma su fitar da ku daga gidajenku ba, lallai Allah yana son masu kyautatawa da kuma sada zumunta)** [al- Muntahana: 8], wannan ɗabi'ar ta bayyana a fili, lokacin da aka zo wucewa da wata gawa ta gabansa, sai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya miƙe saboda ita, sai aka ce masa: Ya Manzon Allah, wannan gawar Bayahude ce fa, sai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Ba rai ba ne?!)**.

Haka ma: girmama manya masu yawan shekaru, da masu matsayi da muƙami, da ba su darajar da ta dace da su, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda bai tausaya wa ƙananan cikinmu ba, bai kuma girmama manyan cikinmu ba, ba shi tare da mu)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ku sanya mutane a matsayinsu)**, lallai wannan ɗabi'a ta bayyana a fili,

lokacin da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya bai wa sahabbai umurnin su miƙe wa Sayyiduna Sa'ad Bn Mu'az (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce masu: **(Ku miƙe saboda girmama shugabanku)**, Sayyiduna Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: **"Abubakar shugabanmu ne, ya kuma 'yanta shugabanmu"**, yana nufin Bilal (Allah ya ƙara yarda da shi). Lokacin da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya tambayi sahabbansa (Allah ya ƙara yarda da su) game da bishiyar da ta yi kama da Musulmi, wadda take fitar da amfani a kowane lokaci da izinin Ubangijinta, kuma ganyayyakinta ba sa faɗi, Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ji a zuciyarsa cewa: dabino yake nufi, kuma amsar tasa daidai ce, sai dai saboda da ƙarancin shekarunsa ya ƙi yarda ya amsa wa Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) a gaban manyan sahabbai guda biyu: Abubakar da Umar (Allah ya ƙara yarda da su); saboda irin yanda yake girmama su, su da sauran manyan sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su).

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai a cikin surorin girmamawa akwai girmama malami, da mutunta shi, da ƙasƙantar masa da kai, da ba shi cikakkun haƙƙoƙinsa, musamman ma ganin cewa addinin Musulunci ya girmama matsayinsa, inda Allah mai girma da buwaya ya gwama shaidarsa, da shaidar mala'iku, da na malamai, Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: **(Allah Maɗaukakin Sarki ya**

**shaida cewa lallai shi ne wanda ya kaɗaita da Allantaka, ya kuma bayyana haka –ta hanyar abubuwan da ya yaɗa a cikin halittu masu ɗauke da dalilai gami da ayoyin da mai hankali ba zai musanta su ba- cewa: shi kaɗai yake, ba shi da abokin tarayya, tsayayye ne shi akan al'amurran halittunsa cikin adalci. Mala'ikunsa tsarkaka ma sun tabbatar da haka, haka ma malamai sun san haka, sun kuma yi yaƙini da shi cewa, Allah Maɗaukakin Sarki shi ne ya kaɗaita da Allantakan da babu wani da zai yi galaba akansa cikin al'amurransa, hikimarsa kuma ta game komai)** [Ali Imran: 18], haka mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Allah yana ɗaukaka darajar muminai masu tsarkake shi a wurin bauta, da waɗanda aka ba su ilimi, duka Allah yana ɗaukaka darajarsu)** [al- Mujadala: 11], Annabimu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai abubuwan da suke sama, da waɗanda suke ƙasa, da kifaye a cikin ruwa suna nema wa malami gafarar Allah, fifikon malami akan mai bauta, kaman fifikon wata daren goma sha huɗu ne akan sauran taurari, lallai malamai magada Annabawa ne)**.

Wani mawaƙi yana cewa:

"Ku miƙe wa malami, ku ba shi cikakkiyar girmar da ta dace da shi; domin malami gaf yake da ya zama Manzo..
Shin kai ka san wanda ya fi daraja da girma sama da wanda yake gina zukata da hankula da samar da su?!"

Lallai muna matuƙar buƙatar yaɗa kyawawan ɗabi'u masu daraja a cikin al'ummarmu, mu mayar da su su zama mana tada da manya da yara, mata da maza suke rayuwa akansu, da su ne al'umma za ta rayu, ta kuma sami ɗaukaka, hakan ne kuma zai gadar da haɗin kai, da cigaba, da samun tsaro da kwanciyar hankali.

**Ya Allah Ubangiji ka shiryatar da mu zuwa ga kyawawan ɗabi'u, ka kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashe.**